# "Qa'idojin Rubutun Hausa, Ga Qoshi Ga Kwanan Yunwa"

**Hauwa Muhammad Bugaje**
Sashen Harsuna da Al'adun Afirka
Jami'iar Ahmadu Bello, Zaria

**Abstract**
Hausa is language that is blessed with a lot of works of scholars on the issue of its orthography and standardization. There is no language in Nigeria that is even close to Hausa in terms of standardization of its orthography. Hausa language was initially written in Ajami after the advent of Islam in Hausa Land, later, Hausa language was also benefitted with modernism and the way of writing brought by colonial masters. The colonial masters and Hausa Scholars introduced the standard way of writing through their publications and conferences in and outside the country. This paper reviews the effort scholars in standardizing Hausa writing, and the problems that are encountered by the users and the students in writing the language especially now with the advent of technology and globalizations. The paper also recommends ways that can be considered in improving good writing among Hausa's especially at the academic level.

**Keywords:** Hausa, Ajami, Islam, standardization

## Gabatarwa

Harshen Hausa yana xaya daga cikin manyan harsunan duniya da aka daxe da sadarwa a cikinsa a rubuce. Rubutu dai kamar yadda masana irin su Bunza (2002) suka tabbatar, ya shafi zayyana ta hanyar amfani da wasu alamomi da nufin sadarwa. A duk inda aka yi maganar sadarwa a rubuce akwai bukatar tsari ko doka da zata yi jagoranci wajen samar da daidaito da fahimtar abin da aka rubuta. Shi kuwa harshen Hausa ya daxe da samun wannan gata na rubuta shi da daidaita rubutunsa a matakai daban daban har zuwa matakin da rubutun Hausa ya samu kansa a ciki a wannan lokaci. Sai dai kuma duk da wannan ci gaba da harshen ya samu har yanzu da sauran rina a kaba, saboda fahimtar qa'idojin rubutu ga xalibai musamman masu nazarin harshen Hausa matsala ce da take yi wa fagen nazari tarnaqi. Wannan takarda ta haska wasu daga cikin matsalolin da suka haifar da koma baya wajen fahimtar qa'idojin rubutun Hausa ga xalibai, tare da hasashen mafita ga wannan matsala.

Kusan a iya cewa babu wani harshe a faxin Nijeriya da aka daxe da rubutuwa kamar harshen Hausa, domin an fara rubuta shi da haruffan Larabci tun bayan shigowar Musulunci qasar Hausa tun wuraren qarni na goma sha xaya (Yahya, 1988). An rubuta Hausa da fitaccen tsarin rubutu biyu waxanda har wannan lokaci ake amfani da su wato rubutun Ajami da na Boko. Waxannan nau'o'in rubutu sun samu karvuwa da kuma samun sauye-sauye a lokuta daban daban, kuma sun kai Hausa qasashe daban daban a faxin duniya. Marubuta na cikin gida da qasashen waje sun bayar da gudummawa wajen inganta rubutun Hausa musamman na boko, sai dai duk da wannan daxewa da aka samu na kasancewar harshen a rubuce, da kuma qoqarin masana wajen daidai rubutun da samar da hanya ta bai xaya ta rubuta shi a faxin duniya amma har yanzu akwai qarancin fahimtar qa'idojin rubutunsa da kuma qarancin ayyuka na yadda za a koyi rubutunsa. Wannan muqala ta fito da wasu daga cikin matsalolin da suke yi wa xalibai tarnaqi wajen koyon rubutun harshen.

## Ma'anar Rubutu da Taqaitaccen Tarihin Samuwarsa

Rubutu suna ne na aikin zayyana ta hanyar amfani da alamomi ko surori ko kuma wasu haruffa da aka amince da su a harshe. Shi dai rubutu qirqirarsa ake yi ta amfani da ilimi

CC BY-NC-ND

domin a fito da hanya karvavviya da za a yi amfani da ita domin sadarwa a zayyane ba a magance ba. (Xavier 1995)

Rubutu yana xaya daga cikin hanyoyin sadarwa da Allah ya hore wa xan'Adam sarrafa shi domin isar da saqo tsakanin mutum da mutum ko tsakanin al'umma da al'umma. Kafin samuwar rubutu, xan'Adam yana sadarwa ne ta hanyar magana, sai dai ita magana tana biyan bukatar sadarwa ta nan take ne, kuma tsakanin mutanen da ke wuri xaya. Samuwar ilimin rubutu ya taimaka matuqa wajen sauqaqa sadarwa tsakanin mutane da isar da saqo cikin sauqi tare da adana bayanai.

Samuwar rubutu ya zo wa xan'Adam mataki-mataki ne tun daga fara rubutu ta hanyar zayyana alamomi da surori na abin da ake so a yi magana a kansa, har aka kai ga matakin amfani da haruffa wato baqaqe da wasula da kuma yadda amfani da wa]annan hanyoyi suka yi ta samun sauye-sauye daga lokaci zuwa lokaci. Kowace al'umma da nata tsarin rubutun, ko dai wanda suka qirqiro ko kuma wanda suka ara daga wasu al'ummomi.
Bincike ya nuna cewa an fara rubutu kusan tun shekaru 50,000 da suka wuce, daga cikin waxanda aka fara samun rubutunsu a wancan lokaci akwai mutanen Sin wato China, waxanda suka qirqiri rubutu a wancan lokaci ta amfani da alamomi na sawun tafiyar tsuntsaye ko surori da kuma alamomi daban daban domin isar da saqonsa

Haka kuma, su ma Sumeriyawa sun da]e da fara rubutu ta amfani da zana surar abin da suke so su yi magana a kansa. Misali sukan sarrafa surori 600 na halittu da alamomi daban daban kamar a inda suke magana a kan doki sai su zana doki ko mutum ko ruwa da makamantan haka. Idan mutum ya ga zanen sai ya harhaxa ya gane saqon da ake so a isar.

Tafiya ta yi tafiya rubutu ya samu har a qasar Misra dubban shekaru da suka shuxe, sai dai su ma kamar Sinawa da Sumeriyawa, a wancan lokaci suna amfani surori da alamomi ne wajen isar da saqo. Idan zaka iya tunawa a baya an bayyana cewa Sumeriyawa na amfani da surori 600 a rubutunsu, su kuma Misrawa suna amfani da surori 700 a wannan nau'in rubutu na zane a waxancan zammuna da suka wuce. Idan aka yi maganar rubutu na haruffa wato rubutun abacada kuwa, bincike ya nuna cewa an fara wannan rubutu ne shekaru 3.400 da suka wuce, kuma Fonisawa ne suka qirqire shi, wato mutanen qasar Phonesia can kusa da Syria. Su kuwa waxannan mutane suna da baqaqe da wasulla 22 da suke amfani da su wajen rubuta harshensu a wancan lokaci, sannu a hankali Romawa suka fahimci wannan tsarin rubutu suka kuma kwaikwaye shi domin rubuta harshensu na Latin, sai dai su suna amfani da haruffa da wasula 23 ne wato sun yi qari a kan na Fonisawa. Tafiya ta yi tafiya, irin waxannan haruffa suna samun karvuwa har zamanin da Turawa su ma suka fahimci wannan tsarin rubutu, suka kwaikwaya domin rubuta harshensu na Turanci. Sai dai ko kafin Turawa su rubuta harshensu da tsarin rubutun 'abacada' Larabawa sun qirqiro rubutun Larabci shekaru 2,000 da suka shuxe wanda duk da cewa rubutu ne na amfani da haruffa da wasulla amma ya bambanta da rubutun 'abacada." (Bunza 2002)

**Rubutun Hausa**

Samuwar rubutu a Hausa yana da ala}a da tarihin samuwar rubutu a duniya. Kamar yadda mawuyacin abu ne a iya kawo lokacin da aka fara rubutu a duniya, sai dai a yi hasashe, haka abin yake a Hausa, domin mawuyacin abu ne a iya tabbatar da sa'adda aka fara rubuta harshen Hausa da kuma salon rubutun da aka fara yi a Hausa. Wannan kuwa bai rasa nasaba da cewa babu wani gagarumin bincike da aka gudanar a wannan fanni na rubutun Hausa. Tabbatacciyar hujja da aka iya fi saurin gabatarwa ita ce wadda take nuna an fara samun rubutu a Hausa bayan shigowar Musulunci qasar Hausa da aron haruffan Larabci aka qirqiri rubutn ajami.

Kodayake an xan samu wasu hujjoji da suke nuna an ta~a rubuta harshen Hausa da harshen Girkanci da kuma yiwuwar rubuta shi da harshen Romanci wato Latin. Wannan bayani ya samu ne ta bakin shararren xan siyasar nan kuma mai da kishin Arewa wato malam Aminu Kano. An bayyana cewa Aminu Kano ya tava ganin wani tsohon rubutu da aka

yi na Hausa da haruffan Girkanci a Ingila wanda ake hasashen an yi shi lokaci mai tsawo da ya wuce. Haka kuma, Aminu Kano ya tabbatar da wanzuwar wata rijiya a Kano da ke xauke da rubutun Romanci a jikinta wanda aka ce an yi tun zamanin daular Romawa. Da wannan ne shi malam Aminu Kano yake hasashen akwai yiyuwar rubuta Hausa tun a wancan lokaci ta amfani da tsarin rubutun waxannan harsuna wato Girkanci da Romanci.

Fitaccen rubutu da ake amfani da shi a Hausa nau'i biyu ne wato rubutun ajami da na boko. Shi dai rubutun ajami rubutu ne da aka ari haruffan Larabci wajen rubuta furuci da maganar Hausa. Shi kuma rubutun boko rubutu ne da ake yi a Hausa ta amfani da haruffan abacada da Turawa suka ara daga Romawa suka rubuta harshensu, suka kuma qirqiri rubutun Hausa a cikinsa.

Rubutun ajami kamar yadda aka bayyana ya samu ne tun bayan shigowar Musulunci da fahimtar ilimin addini a qasar Hausa a wuraren qarni na 15 ko na 16 har suwa na 17. Irin wannan rubutu ya sami karvuwa da bunqasa musamman a qarni na 18 zuwa na 19 har ma cikin qarni na 20.

Malaman addinin Musulunci da waxannan qarnoni irin su malam Abdullahi Suka da malam Abubakar ibn Kutun-kura da sheik Ahmed Tila da sauransu suna daga sahun farko na malaman da suka yi wa Hausa gata wajen rubuta da babbaqun Larabci tun a qarni na 17. Masu biye masu wajen wannan aiki sune shararrun malaman addinin nan kuma marubuta waqoqin addini na qarni na 18 su malam Shi'itu xan Abdurra'uf da Muhammadu na Birnin Gwari da sauransu, su ma sun bun}asa rubutun Hausa cikin ajami a qoqarinsu na koyar da addinin Musulunci a qarnin da suka rayu. Har ila yau, tarihin rubuta Hausa cikin ajami ba zai kammala ba sai an yi la'akari da gagarumar gudummawar da malamai masu jihadi wato su sheik Usmanu Xanfodio da qaninsa Abdullahi Fodio da xansa Muhammadu Bello da autansa Isan Kware da 'yarsa Nana Asma'u da almajiransa irin su Muhammad Tukur da sauransu da ma masu biye masu irin su Attahirun Amadu suka bayar wajen yaxa addinin Musulunci da samar da rubutu a cikin Hausa a fannoni daban daban na ilimi. Haqiqa ba domin gudummawar waxannan bayin Allah ba da rubutun Hausa ya ji kunya, (Yahya, 1988).



## Haruffan Ajami

Shi kuwa rubutun Hausa da baqaqen boko ya samu ne ta hanyar qoqarin Turawan mulkin mallaka waxanda suke cike da qishirwar gudanar da mulkin mallaka a wancan lokaci. Shi kuwa mulki ba zai yi sauqi ba sai da sadarwa tsakanin waxanda ake mulka da masu mulki. Ita kuwa wannan sadarwa ba zata samu inganci ba har sai an sami hanya mafi sauqi wajen isar da ita. Wannan hanyar kuwa ita ce ta rubutu da tsarin da mai mulki zai fahimta kuma a tilasta wa wanda ake mulka ya koya. Wannan shi ya sa Hausa ta tsinci kanta a rubutun boko.

Kafin qoqarin da Turawan mulkin mallaka suka yi na rubuta Hausa da haruffan abacada, akwai waxanda ake hasashen sun fara assasa wannan rubutu a Hausa lokaci mai tsawo da ya wuce. Wasu daga cikin irin waxannan ayyuka sune waxanda aka ji xuriyarsu a 1773 sa'adda aka samu wasu fatake 'yan kasuwa suka haxu da wani bawa na wazirin Tunis Abdurrahman wanda aka ce ya rubuta wasu kalmomi na Hausa da haruffan abacada waxanda suka haxa da:


Ghal - gari
Dudsji – dutse
Korama – korama
Ghurasa – gurawa

Haka kuma, bincike ya nuna cewa a 1790 an wallafa bayanan wani falke xan kasuwa

bahaushe mai suna El-haj Abdusalam a Ingila. Haka kuma, wani ma'aikacin African company mai suna T.E Bowdich ya ziyarci Ghana (Kumasi) har ma ya rubuta kalmomin qidaya guda 20. (Bunza 2002:32)

Haka aka yi ta samun xaixakun rubuce-rubucen Hausa a shekarun da suka gabata har lokacin da Turawan mishan da na mulkin mallaka suka duqufa wajen rubuta Hausa cikin rubutun abacada. Turawan mulkin mallaka sun yi qoqarin rubuta Hausa a tsarin rubutun boko tun bayan da suka sami kama akalar qasar har zuwa lokacin da suka shimfixa mulkin mallaka. An kafa makarantar farko da za a koyar da rubutu da karatu a Kano, kuma aka xora wa baturen da ke kula makarantar mai suna Hans Vitcher xawainiyar samar da baqaqe da haruffan abacada da suka dace da rubuta Hausar. Har ila yau, an duqufa wajen samar da litattafai cikin Hausa da zasu taimaka wajen koyo da koyarwa. Wannan yunquri ya haifar da kafa hukuma fassara wadda ta Fassara litattafai cikin Hausa, da hukumar Talifi wadda ta jagoranci samar da qagaggun labarai na Hausa da za a yi amfani da su wajen karatun Hausa.

A taqaice za a iya cewa an samar wa da Hausa haruffan abacada 30 da ake amfani da su wajen rubutu. Daga cikin waxannan haruffa akwai na gwauraye da masu goyo wato waxanda ake samu a harshen Turanci da kuma waxanda aka qirqira domin biyan bukatar harshen Hausa na rubuta furucin da a harshen kaxai ake samu ba su a Ingilishi.



**Hoton Haruffan Abacada na Hausa**

## Qa'idojin Rubutun Hausa

Qa'idojin rubutu xawainiya ce da masana suke yi ta daidaita rubutu da samar wa al'umma matsaya a kan yadda za a rubuta harshe. Ma'anar daidaita rubutu kuwa na nufin yin rubutu daidai da fahimtar kowane xan asalin harshe da ma mai koyon harshen. Akan kira rubutu daidai idan ya hau tsarin da masana suka shimfixa kuma hukuma ta aminta da shi.

Amin (2016:62) ya bayyana cewa qa'idar rubutu yarjejeniya ce tsakanin masana harshe da ake cim mawa domin a samar da tsarin rubutu na bai xaya. Haka kuma, ya qara da cewa qa'idojin rubutu sun shafi yadda ake rubuta kalma da yadda ake amfani da manyan baqi da qanana, da karan-xori da kuma yadda ake sarrafa alamomin dakatarwa da samun daidaito a kan karin harshen da ya dace da rubutu.

## Samuwar Qa'idojin Rubutu a Hausa

An daxe ana rubuta Hausa da baqaqen boko ta hanyoyi daban-daban kafin a cim ma yarjejeniya wajen tabbatar da qa'idojin da ake bi a yanzu. Akwai abubuwa uku da suka sha wa masu qirqirar rubutun Hausa na boko a wancan lokaci. Waxannan abubuwa kuwa sun haxa da matsalar furucin baqaqen da ba a su a harshen ingilishi wato irin su x da q da 'y da ts da gw da fy da ky da kw. Haka kuma matsala ta biyu ita ce ta yadda ya kamata a haxa kalma da kuma inda ya kamata a raba kalma. Har ila yau ga kuma matsalar karin harshe da yadda ake samun bambanci wajen wasu kevavvun kalmomi da suke da bambanci a kare-karen harshen Hausa, wane ya dace a xauka a yi amfani da shi? Kuma ya za a yi ya sami karvuwa ga sauran 'yan asalin harshen da basu da wannan kalma? Da haka aka soma tattauna

CC BY-NC-ND

waxannan matsaloli har aka cim ma samar da daidaito na qa'idar da ta dace.

Kafin a sami qa'idojin rubutu, yadda ake rubuta Hausa a wancan lokaci (kafin qarni na 20) ya sha bamban da yadda ake rubuta Hausa a yau, kuma kusan kowane marubuci da dabararsa. Misali an sami wani littafin J.F Schon (1885) mai suna *Magana Hausa*, inda ya rubuta wasu kalmomi da wasu xige-xige a qarqashin wasu wasulla, da kuma wasu alamomi masu nuna karin sauti na wasu kalmomin, har ma da haxa kalmomin da a magance ko a rubuce bai kamata a haxe su ba, misali a inda ya rubuta *tasi* a madadin *tashi*, da sanu a madadin shanu, da kuma *acikin* a madadin *a cikin.* Shi ma C.C H Robinson mai Qamus na Nahawun Hausa da Frank Edgar mai littafin tatsuniyoyi na Hausa duk sun yi amfani da xige-xige ga haruffan da ba Ingilishi, kuma sun rubuta wasu kalmomin yadda suka fahimce su, ba yadda xan asalin harshe yake faxi ba. (Yahaya 2002:124)

Kamar yadda aka gani rubutun boko na Hausa na farko ya fara da matsala saboda ba 'yan asalin harshen suka fara rubuta shi ba. Wannan dalili ne ya sa daga bisani aka kawo masa xauki da nufin samun daidaito da fahimta ta bai xaya. Daga cikin waxanda suka bayar da gudummawa akwai Hans Vischer ([an Hausa) da Bargery G.P (1934) da Dr. R.M East da sauransu (ta vangaren Turawan mulkin mallaka). Haka kuma akwai ayyukan hukumar daidaita harshen Hausa wadda ta shirya tarurruka da dama domin kulawa da qa'dojin rubuta Hausa. Daga ciki akwai taron da aka yi a 1966 a Bamako ta qasar Mali da kuma wani taron da aka sake yi a jami'ar Ahmadu Bello da ke Zaria a 1970 da kuma wanda aka yi a Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya da ke Kano a 1972. Haka dai aka ci gaba da kawo wa rubutun Hausa xauki har rubutun ya kai ga matakin da yake a yau.

## Koyon Qa'idojin Rubutun Hausa

Masu iya magana kan ce "icce tun yana xanye ake lanqwasa shi..." koyon qa'idar rubuta Hausa tana farawa ne tun lokacin da xalibi yake a qaramar makarantar firamare, wato tun sa'adda aka fara share qasa ana rubuta masa harrufa yana kwaikwaya. Daga wannan mataki ne yaro zai fahimci haruffan Hausa da siffofinsu. Idan xalibi ya kiyaye yadda zai zana su a cikin rairayi sai, a samar masa da qaramin allo ya yi ta gwada rubuta su, kana daga bisani a saya masa littafin rubutu mai jan layi wanda zai riqa rubuta haruffa da kalmomi yana kuma maimata rubuta su har sai ya kiyaye da inda ake haxa kalma da inda ake raba kalma da kuma yadda ya dace da rubuta sunaye da sauran dokokin rubutu. Duk wannan hidima qwararren malami ne yake yinta cikin kulawa da sha'awa, sa'annan da taimakon iyaye wajen bita da duba aikin gida.

Duk abin bai tsaya a nan ba, sannu a hankali xalibi zai kiyaye rubutu har ya kai ga yana shaida waxannan qa'idoji a wajen rubutun insha'i. Haka kuma, litattafan da hukuma ta tanadar na koyar da harshen Hausa duk sun tanadi matakai daban daban na koyon rubutun tun daga kan littafin *Mu koyi karatu* da *Mu yi karatu* da na *Hausa don qananan makarantun Sakandare* da sauransu duk jagorori ne na koyon kyakkyawan rubutu. Ashe ba banza ba a da aka yi haziqan marubuta irin su Abubakar Imam da su Aminu Kano da gogaggun 'yan jarida masu iya sarrafa Hausa irin su Halilu Ahmad Getso da sauransu.

"Kowa ya tuna bara, bai ji daxin bana ba." mutum nawa zai iya tunawa da wannan tsarin? Shin ko hakan yake wakana a yau? Amsar waxannan tambayoyi su zasu kaimu ga batu na gaba wato matsalar fahimtar qa'idar rubutun Hausa.

## Matsalolin Fahimtar Qa'idojin Rubutun

Kamar yadda aka bayyana a baya cewa bin qa'ida yayin rubutu shi yake samar da ingancin rubutu har ya yi daxin karantawa. Haka kuma, fahimtar qa'idojin rubutu ya ta'allaqa ga sanin muhallan da ya kamata a haxa kalma, da inda ya dace a raba kalma da sanin yanayin gavovin kalmomi da kuma yadda ake xauri da yadda ake sarrafa alamomin rubutu a cikin rubutu da har ma da tsarin ginin jumla da dai sauransu.

Rubutun Hausa a wannan zamani yana fuskantar naqasu saboda matsalar da ake fama da ita ta kasa kiyaye qa'idojin rubutu. Idan

akwai waxanda ya kamata su fi kowa kiyaye waxannan qa'idoji sune xalibai masu nazarin harshen, saboda su ake horarwa da nufin zama malaman Hausa da 'yan jarida da marubuta da mafassara da sauran fannoni na ayyukan da al'umma take bukatar qwarewarsu. Sai dai kuma, fahimtar waxannan dokoki ko qa'idoji da kiyaye su yayin rubutu suna haifar da gazawa ga waxannan xalibai. Daga cikin matsalolin da suka haifar da rashin kiyaye qa'idojin rubutu ga xalibai sun haxa kamar haka:

- **Rashin Qwararrun Malamai Masu Koyar da Hausa a Matakin Firamare**

Makarantar farko da kan fara koyar da xalibi iya rubutu da karatu ita ce makarantar Firamare. A wannan mataki ne ake koyar da yara baqaqe da wasulla da kuma yadda zasu haxa kalma. Kafin yaro ya kammala Firamare ya cancanci a ce ya iya kyakkaywan rubutu har ma da iya karanta shi. A da akan sami xalibin Firamare ya rubuta gajeren labari da Hausa kuma cikin kyakkyawan rubutu. Amma wannan batu ba haka yake ba a makarantun Firamare a yau, hasali ma makarantu masu zaman kansu suna ganin rashin wayewa ne koyar da harsunan gida irin su Hausa a makarantunsu, sai dai a koyar da harshen Turanci da Faransanci da wasu harsunan da ake gani burgewa ne yaro ya iya su. Idan har aka yi sa'a aka sami makarantar da ta yarda da koyar da Hausa, za a tarar cewa wani malami ne da ake zaton ya iya magana da Hausa za a sa ya koyar ba tare da la'akari da qwarewarsa a wannan fage ba. Su kuwa makarantun gwamnati ba a cewa komai, domin mafi yawan xaliban da suke yayewa ko sunansu da qyar suke iya rubutawa ba ma maganar iya rubutu da karatu ba.

- **Rashin Kulawar Hukumomin Ilimi**

Rashin kulawar hukumomin ilimi ya taimaka wajen kawo cikas ga koyon rubutun Hausa. Da a ce hukuma tana tabbatar da dokar nan na koyar da karatun Firamare da qaramar Sakandare da harshen uwa da an sami kulawa ga koyon rubutun Hausa. Haka kuma, hukumomin ilimi suke da alhakin kula da malamai da tabbatar da cewa sun cancanta kafin a xauke su aikin koyarwa.

- **Rashin Sha'awa da Mayar da Hankali daga Xalibai**

Mafi yawa xaliban Hausa suna wa karatun Hausa kallon qawalwaniya ne, wato saboda harshensu ne na asali, ba sa bukatar su dage wajen koyonsa, domin suna hasashen cewa ko jarabawa aka zo zasu iya rubutawa kuma su ci. Sai dai abin ba haka yake ba, domin harshe a magance daban yake da harshe a rubuce. Idan har aka zo fagen nazari ana bukatar nuna sha'awa da jajircewa da kuma mayar da hankali domin a fahimci tsarin dokokin nazarin harshen.

**5.1 Mafita**

- Samar da sababbin hanyoyi na zamani na koyar da rubutun Hausa
- Daukar qwararrun malamai
- Sanya gasa a matakai daban daban da za mayar da hankali a kan qa'idojin rubutu
- Bayar da muhimmanci a kan iya rubutu yayin jarrabawar daukar dalibai a matakin gaba da sakandare
- Qirqirar sabbin kwasa-kwasai da za su sa dalibai su goge a harkar rubutu a manyan makarantu.

## Manazarta

Amin, M.L (2016), "Waiwaye Adon Tafiya: Sake Bitar {a'idojin Rubutun Hausa." *Harshe 9, Journal of African Languages*, Zaria: Dept of African Languages and Cultures, Ahmadu Bello University.

Bunza, A. M. (2002). *Rubutun Hausa Don Masu Koyo Da Koyarwa*. Lagos: Ibrarash Islamic Publications Centre LTD.

Galadanci, M.K.M. (1976), *An Introduction to Hausa Grammar*. Zaria: Longman.

Kraft C. H. and Kirk-Greene A.H.M. (1990).*Teach Yourself Hausa. A Complete Course for Begnners*. London: Hodder and Stoughton Ltd.

Sani M. A. Z. (1999).*Tsarin Sauti da Nahawun Hausa*. Ibadan: University Press Plc.

Skinner, N. (2007).*A Grammar of Hausa for Nigerian Secondary Schools and Colleges*. Zaria: Northern

CC BY-NC-ND

Nigerian Publishing Company.
Wikipedia: https://en.wikipedia.org/wiki/Orthography
Wurma, A. G. (2005).*Daidaitacciyar Hausa da {a'idojin Rubutunta*. Kaduna: Olatunde Rasheed Publishing Works.
Yahaya, I. Y. (1988). *Hausa A Rubuce: Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa*. Zariya: Northern Nigerian Publishing Company Ltd.
Zaria, A. B. (2014).*Sabon Nahawun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press Plc.
Zarruq, R. M. (1978).Tarihin {a'idojin Rubutun Hausa (Ed) Yahaya, I. Y. and Rufa'i, A.*Language and Literature in Hausa* Kano: Uniprinters Limited.
https://scholarspace.manoa.hawaii.edu/bitstream/handle/10125/24625/roberts.pdf